# Ninth Round Student Report a Project Essay Competition February – March 2020

Report on Abandoned Projects/Poorly Done Projects

Name: Nafisa Muhammad Aliyu

Institution: Kano State Polytechnic

Department: Statistics

School Reg. No: ND/STA/17/085

Level of Student: II

Project Title: Aikin Titin Bela, Dakata

Project Location: Bela, Dakata Kano

Project Start Year: 2004

Project Abandoned Year: 2006

Level of Completion of the Project: 10%

Aikin titin Dakata zuwa Bela, aiki ne wanda ya dade ana fama dashi amma har yanzu ba'a cigaba da wannan aiki ba, aikin an fara shi a shekarar 2004, a zamanin me girma Gwamnan Kano Mallam Dr. Ibrahim Shekarau, wanda tun lokacin da aka tsaya da wannan aiki babu wata gwamnati da ta ci gaba da wannan aiki, a shekarar 2015 mai girma Gwamnan Kano, Dr. Abdullahi Umar Ganduje yayi alkawarin ci gaba da wannan aiki wanda har yanzu shiru, wai Mallam yaci Shirwa, a halin da ake ciki yanzu ana fama da yawan mace mace sakamakon hadarurruka da ake samu sanadin wannan hanya, wani abu ban tausayi ma agaresu shine yanda koh mutuwa akai bamu da hanyar kai gawa makwancinsa sai mun biyo ta ciki ruwa a lokutan Damuna.

Mai girma Gwamna, Al'ummar wannan yanki suna dora yaqininsu akan cewan kai mai taimakaon talakawa ne, musamman su da suke neman taimako, mai girma Gwamna matsalar Titin Bela kullum qaruwa take, kuma kasan titin nan shine

rayuwar mutanen wannan yanki gaba daya, da kuma ta iyalinsu, bisa dogoro da cewar sai suna dashine zasu wuri aiki, da kuma kai yara makaranta, akan lokaci, mai girma Gwamna hanyar nan a yanxu ba karamar barazana ce ga mutanen wannan yanki ba, shi yasa na rubuta wannan report da taimaka Centre for Information Technology and Development (CITAD), don janyo hankalin gwamnati akan ganin an ceto wannan hanya domin cigaban al’ummar wannan yanki da al’ummar Kano gaba daya, da fatan wannan report zeje kan teburinka, kuma za’a duba abin don wannan gwamnati ta jama’a kuma don jama’a.

**Nafisa Muhammad Aliyu**
School of Technology, Kano State Polytechnic

Pictures were taken during rainy season 2019







